Bijochs: Dec, 2025 Vol. 3 - Issue, 2 ID No. 002 (Pg.16-23))

# Matsayin Hausa da Kalubalen da Yake Fuskantarta a Yau

**Dr. Hauwa Muhammad Bugaje**
hhmbugaje@gmail.com
Sashen Harsuna da Al'adun Afirka
Tsangayar Fasaha,
Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya

***Tsakure***

*Wannan muƙala ta ƙunshi tsokaci game da halin da Hausa ta sami kanta a wannan zamani. An yi ƙoƙarin fito da matsayin Hausa ta fuska huɗu; ta fuskar harshe da al'umma da ƙasa da kuma hikima ko azanci. Haka kuma, muƙalar ta yi amfani da ra'ain Zahiranci wajen nazarin abubuwan da suke faruwa da Hausa a yau, waɗanda suka ɗaga martabarta da waɗanda suka zamar mata ƙalubale. A ƙarshe, an kammala muƙalar da bayar da shawarwari dangane da hanyoyin da ake sa ran idan an bi su, za a shawo kan matsaloli ko ƙalubalen da yake damun Hausa wanda ya haɗa da rashin kula da 'yan asalin harshen suke nuna wa harshen da ƙarancin nazarinsa a makarantu da halin da ƙasar Hausa take ciki na rashin tsaro da kuma uwa uba sakin kyawawan ɗabi'u da al'umma suka yi.*

***Keɓaɓɓun Kalmomi:*** *Hausa a Yau, Kalubale.*

## 1.1 Gabatarwa

Hausa harshe ne da Allah ya yi wa baiwa mai yawa, kuma ya ɗaukaka shi a tsakanin harsuna sa'o'insa. Haka kuma harshe ne da yake da sauƙin koyo da sadarwa, kuma al'ummarsa tana da sauƙin kai da karɓar baƙi har ma ta yi masu abin nan da masu iya magana kan ce "hankaka mai da ɗan wani naka." Haka kuma, kamar yadda al'ummar take da ɗabi'ar karɓar baƙi, haka a kullun rana take karɓar baƙin kalmomi, take taskace su tare da sauya masu siga domin su dace da tsarin harshen ta yadda ko an mayar wa masu kalmar ta asali ba zasu gane cewa ta su ba ce. Haka al'amarin harshen Hausa yake kasancewa a kowane ɓangare na rayuwa da kuma kowane yanayi, harshen ya sami kansa a ciki ba ya baƙunta kuma baya jinkiri wajen karɓar ɓaƙin al'amurra da hausantar da su.

Idan muka koma ga al'umma, a yau mawuyacin abu ne ka iya ware ƙabila ɗaya tilo a matsayin Hausawa, hasali ma Hausa ta tashi daga ƙabila ta koma al'umma da ta haɗa ƙabilu da dama a cikinta. Wannan dalili ya sa har yau masana suke ta kai ruwa rana wajen gano wane ne Bahaushe na asali, kuma wa zai amsa sunan Bahaushe a yau? Wannan muƙala ta bijiro ne da nufin waiwayen matsayin Hausa a duniya, wato tafiyar da ta yi na nisan zango da nasarorinta da kuma matsayinta a yau da ƙalubalen da suke fuskantarta. An yi amfani da wasu rubutattun waƙoƙi domin kafa hujja a bayanan da aka kawo. Wannan muƙala ta kammala da shawarwari da zasu zama mafita ga Hausa da Hausawa a nan gaba.

## 2.1 Ma'anar Hausa

Kalmar Hausa kalma ce mai bakandamiyar ma'ana, wato kalma ce da ma'anarta ba ta tsaya ga abu ɗaya tilo ba. Hasali ma idan aka tashi bayar da ma'anar Hausa, ana la'akari da abubuwa da dama da suka haɗa da harshe da al'umma da ƙasa da kuma hikima ko azanci ko dabara duk zasu iya ɗaukar ma'anar Hausa. Hausa takan ɗauki ma'anar harshe, wato yaren da al'ummarta suke amfani da shi. Haka kuma takan ɗauki ma'anar sassauƙan harshe wanda bahaushe zai iya fahimta, (idan an yi masa maganar da ba ya fahimta, yakan ce a yi masa da hausa, wato a fahimtar da shi). Har ila yau, Hausa tana ɗaukar ma'anar al'umma, wato mutanen da suke magana da ita, akan kira namiji tilo da bahaushe, mace tilo kuma bahaushiya, jam'insu kuma Hausawa. Har ila yau, Hausa tana nufin ƙasa wadda al'ummar Hausawa suke rayuwa a cikinta a matsayin ƙasarsu ta asali. A ma'ana ta ƙarshe a wannan muhallin ita ce, Hausa na nufin azanci ko dabara ko hikima, domin idan mutum ya yi wani abu ba daidai ba akan ce masa ba ya da hausa, ma'ana ba ya da azancin da zai yi daidai. (Bargery, 1934: 459).

Vycichl W. (1934), ya bayyana cewa har zuwa lokacin bincikensa ba a samu wani aiki da ya nuna tushen kalmar Hausa ba, sai dai 'yan asalin harshen suna kiran kansu da; 'ba-haushe' ga tilo kuma namiji, ba-haushiya' ga tilo kuma mace, sai kuma jam'i Hausawa. Sa'annan suna kiran harshen da hausanci ko hausa.

## 3.1 Matsayin Hausa ta fuskar Harshe

Harshen Hausa ɗaya ne daga cikin manyan harsuna na tafkin Chadi wanda ake samu a farfajiyar yammacin Afirka. 'Yan uwansa na jini kuma na yammacin Chadi sun haɗa da Gwandara da Bade da Dass da Bole da Angas da Kare-kare da sauransu. Harshen Hausa harshe da yake da mafi yawan jama'a da suke amfani da shi a faɗin Afirka, domin ƙididdiga ta masu ƙididdiga ta 2025 ta nuna akwai kimanin mutane miliyan 150 zuwa miliyan 200 da suke amfani da harshen Hausa a faɗin duniya. Haka kuma, masu jeranta harsunan duniya sun bayyana harshen Hausa a matsayin harshe na goma sha ɗaya a jerin harsunan duniya ta la'akari da yawan jama'a. Har ila yau, harshen ya yi gagarumar nasara na samun daidaitaccen tsari da ƙa'idojin rubutu tun zamanin Turawan mulkin mallaka. Kodayake tarihin rubuta Hausa ya faro ne tun kafin zuwan Turawa, domin an daɗe da rubuta shi cikin kyakkyawan tsarin rubutun ajami.

Matsayi da ɗaukakar harshen Hausa ya sa aka zaɓe shi a matsayin harshen sadarwa a tsakanin sojojin Afirka ta yamma a zamanin yaƙin duniya na biyu. Wannan kuwa ya faru ne saboda sauƙin koyo da harshen yake da shi, da sauƙin sadarwa da ake samu a cikinsa. Aƙilu Aliyu yana cewa:

> Harshen Hausa ya ƙasaita,
> Harshen Hausa ya gawurta,
> Harshen Hausa ya wuce tsara.
> (Aƙilu Aliyu; waƙar Harshen Hausa)

Har ila yau, ƙasaitar harshen Hausa ta sa ya kafu a kafofin watsa labarai na gida da ƙasashen waje waɗanda suka ɗauki shekaru masu dama suna gudanar da shirye-shirye cikin harshen Hausa. Tashoshi irin su BBC

Hausa da Muryar Amurka da Radio Jamus da Radio China da TRTHausa da sauran manyan kafofin watsa labarai sun jima suna cin gajiyar Hausa wajen watsa labaransu. A cikin gida kuma akwai tashoshi irin su Radiyon Tarayya ta Kaduna da Radiyo Nagarta da Alheri Radiyo da ɗinbin tashoshi na Radiyo da talabijin da suka daɗe da watsa shir-shiye cikin Hausa. Kafofin sadarwa na zamani ma irin su Facebook sun sami tagomashin harshen Hausa domin harshe ne da aka fi sadarwa da shi a kafafen sada zumunta na zamani fiye da sauran harsunan Nijeriya.

Haka kuma, harshen Hausa ya sami kai wa ga matsayin harshen ƙasa a Nijeriya, wato yana ɗaya daga cikin manyan harsuna uku da aka amince da amfani da su a wajen koyarwa musamman a matakin Firamare zuwa ƙaramar Sakandare, kuma za a iya amfani da shi a kotuna da a zaman majalisun jihohi. Haka kuma, harshe ne na sadarwa a wuraren ibada kamar masallatai da majami'u da kuma cinikayya a kasuwanni. Har ila yau, harshen ya kasance harshen ƙasa kuma harshen hukuma a jumhuriyar Nijar, wato za a iya amfani da shi wajen gudanar da ayyukan gwamnati da sauran al'amurra da suka shafi ƙasa.

### 3.2 Matsayin Hausa ta fuskar Ƙasa

Ƙasar Hausa ƙasa ce da take a arewacin Nijeriya da kudancin Nijar. Ƙasa ce da ta ƙunshi dauloli masu daɗaɗɗen tarihi kamar daulolin Katsina da Kano da Daura da Zazzau da Gobir da Kabi da Zamfara da Maraɗi da Damagaran. Jihadin daular Usmaniyya ya dunƙule waɗannan dauloli a matsayin daula ɗaya wato daular Usmaniyya wadda mujaddadi Shehu Usmanu Ɗan Fodiyo ya kafa. Dangane da yanayin ƙasa kuwa, ƙasar Hausa ƙasa ce yalwatacciya, wadatacciya, ni'imtacciya mai ƙunshe da ɗimbin arziki a ƙarƙashinta. Ƙasar Hausa tana da manyan dazuka biyu, wato dajin Sahel mai ƙarancin itatuwa da rairayin hamada, da dajin Sabana, mai duhuwar itatuwa. Haka kuma, akwai yanayi na noma iri biyu, wato rani da damina. Yanayin rani a ƙasar Hausa lokaci ne na noman kayan lambu, yayin da yanayin damina kuma ya dace da noman hatsi da kayan lambu baki ɗaya. (Bunza, 2019)

Dangane da mazaunin Hausawa na asali kuwa, Ɓycichl (1934), cewa ya yi ta samo asali ne daga yankin Azbin inda ƙabilar Tuareg suke, amma yaƙe-yaƙen ƙabilun da suke wannan wuri irin su Banu Hilal da Sulaim, ya sa Hausawa suka yi ƙaura suka nausa Damagaran har zuwa masarautar Bornu suka kafa dauloli a yankunan sahara. A ra'ayin Bakura (2019:14), ƙasar Hausa ta asali ta faro ne daga Lalle da Asodu a arewa maso gabashin Agades, sa'annan ta yi iyaka da gaɓar kogin Kwara daga yamma zuwa ƙasar Dohomey, sa'annan ta yi iyaka da ƙasar Bornu daga gabas, sai kuma daga kudu ta yi iyaka da ƙasashen ƙabilun Bauchi.

### 3.3 Matsayin Hausa ta fuskar Al'umma

Masana sun yi ta bincike da ƙoƙarin gano Bahaushe na hasali, amma abin ya ci tura har yau kasancewar al'ummar Hausawa al'umma ce tumbin giwa a yau, domin al'umma ce da ta haɗa jinsi daban daban na mutane suka dunƙule a matsayinsu na masu magana da harshen Hausa kuma suke amsa sunan Hausawa. Daga cikin ƙabilun da suka zo ƙasar Hausa, suka yi tsawon zamani har suka rikiɗe suka zama Hausawa duk kuwa

da cewa za a iya ganin kamanni na ƙabilarsu ta asali amma an aminta da kasancewarsu Hausawa, akwai Fulani da Bare-bari da Mallawa da Gwanjawa da Yarbawa da Nufawa da Azbinawa da Buzaye da sauransu. (Ibrahim, 2018).

Babban abin da ya haifar da wannan sajewa da rikiɗewa da waɗannan al'ummomi suka yi kuma suke amsa sunan Hausawa a yau, ba ya rasa nasaba da ɗabi'ar karrama baƙi da kyawawan al'adu da kyakkyawan tsari na zamantakewa da kowa zai yi sha'awa da ba kowa damar neman arziki ba tare da hasada da ƙeta ba. Kodayake mafi yawa daga waɗannan al'ummomi al'ummarsu ta asali tana nan, kuma tana amsa sunanta, amma wasu daga cikin 'ya'yanta da harshen Hausa ya zamo harshen farko a wajensu sun fi alaƙanta kansu da Hausa fiye da harshensu na asali.

Al'ummar Hausawa mutane ne masu kyakkyawan tsarin zamantakewa wanda ya fara tun daga gida zuwa unguwa zuwa gunduma zuwa yanki na masarautun hakimai har zuwa ga ƙasa da sarakuna suke jagoranta duk bisa tsari suke tafiya. Haka kuma, kowace sana'a da kuma kowane rukuni na al'umma suna da wakilci a tsarin sarautun Hausawa. Wannan ya kawo zaman lafiya da fahimtar juna a tsakanin al'umma musamman a baya da wannan tsari yake da inganci.

Kyawawan ɗabi'u su suke wa al'ummar Hausawa jagoranci a rayuwa, wato al'umma ce da ta bayar da muhimmanci ga tarbiyya, musamman abin da ya shafi riƙo da gaskiya da biyayya ga na gaba da haƙuri da juriya da kuna da kawaici da kara da zumunci da sauransu. Wannan dalili ya sa har Turawa suke sha'awar wannan al'umma da ganin ƙimarta.

A yau, al'ummar Hausawa sun fantsama a faɗin duniya domin kusan kowane sashe aka shiga a faɗin duniya za ka iya samun Bahaushe ko mai magana da harshen Hausa. Haka kuma, wannan al'umma ta yi kaka-gida a wasu daga cikin ƙasashen yammacin Afirka da suka haɗa da Ghana da Kamaru da Chadi da Senegal da Sudan da Mali da sauransu. Yawan Hausawan da suke a waɗannan ƙasashe ya sa a yau ake bukin ranar Hausa ta duniya a waɗannan ƙasashe. Haka kuma, wasu daga cikin waɗannan ƙasashe suna la'akari da Hausawa a matsayin al'ummomin da suke da tasiri matuƙa a harkokin tattalin arziki da siyasar ƙasashen. A yau matsayin wannan al'umma ya ɗaukaka a idon duniya ta fuskar yawan jama'a da siyasa da tattalin arziki musamman idan aka yi la'akari da mutumin da ya fi kowa kuɗi a Afirka, Bahaushe ne ɗan asalin ƙasar Kano Alhaji Aliko Ɗangwate.

### 3.4 Matsayin Hausa ta fuskar Hikima/Azanci/Dabara

Idan ana maganar Hausa musamman a wajen Bahaushe, abin da zai zo zuciyarsa shi ne hikima da azanci da dabara.Samun waɗannan a tattare da mutum yake sa a kira shi bahaushe. idan kuma aka yi rashin sa'a aka rasa su ga mutum, sai a kira shi da bagwari. Hausawa suna koya wa yaransu hikima da azanci da dabara tun suna ƙanana, ta hanyar tatsuniyoyi da kacici-kacici da almara da hikaya da ƙissoshi masu ɗauke da darussa daban daban na rayuwa. Haka kuma, akan koyar da yara azancin magana kamar karin magana da kirari da salon magana da

sauransu. Haka kan sa yaro ya tashi da basira da naƙaltar harshe. Har ila yau, wasanni na gargajiya irin su wasan wuta da langa da kalankuwa da wasannin tashe suna ƙara kaifafa hikima da azancin 'ya'yan Hausawa da horar da su makamar shugabanci da dabarun jarunta da kare kai da sauran kyawawan al'adu.

### 4.1 Kalubalen Hausa a Yau

Kowane harshen a duniya ba ya rasa ƙalubale ko matsalolin da yake fuskantarsa. Hausa a yau tana fuskantar matsaloli da dama waɗanda suke nema su zame mata tarnaƙi ko ƙarfen ƙafa wajen kai wa ga matakin da take hari. Masana da irin su Amfani (2013) sun bayyana matsayin Hausa a wannan ƙarni da muke ciki, wato ƙarni na ashirin da ɗaya cewa harshe ne da zai iya wakiltar harsunan Afirka a matsayin harshen hukuma, musamman idan aka yi la'akari da yadda harshen yake bunƙasa a kullun, kuma ake ƙara samun yawan masu magana da shi. Sai dai kuma, duk da wannan kyakkyawan hasashe da ake da shi game da harshen, yana fama da ɗimbin matsaloli da zasu iya zama cikas ga harshen musamman idan ba a ɗauki matakin shawo kansu ba.

#### 4.1.1 Kalubalen Harshen Hausa

Harshen Hausa yana cikin yanayin nan da masu iya magana kan kira da "ga ƙoshi ga kwana da yunwa." Abin nufi a nan, a baya an bayyana cewa harshen ya yi wa sauran harsunan Afirka zarra dangane da yawan masu magana da shi, amma kuma ana samun koma baya a kan nazarinsa musamman a makarantun Nijeriya. A baya, darasin Hausa yana ɗaya daga cikin darussan da kowane ɗalibi a makarantun arewacin Nijeriya yake yi, hasali ma malamai sukan mayar da hankali wajen koya wa yara karatun Hausa kafin su iya karatu da Ingilishi. Kusan a matakin Firamare ake koyon karatun litattafan adabi irin su Magana Jari ce da Ruwan Bagaja da Shaihu Umar da sauransu. Haka kuma, akan ci gaba da mayar da hankali wajen koya rubutun Hausa da sa sha'awar karance-karance na litattafan Hausa da jaridu har zuwa matakin jami'a. A shekarun baya har alawus na musamman ake ba malaman Hausa domin ƙarfafa masu gwiwa wajen koyarwa. A yau wannan batu ya sauya, ana samun rashin sha'awar darasin ga ɗalibai, kuma mafi yawa daga makarantu masu zaman kansu ba sa koyar da darasin Hausa musamman ga ɗaliban babbar Sakandare masu karantar kimiyya da fasaha. Wannan ƙalubale ya shafi har karatun jami'a, domin a 'yan shekarun nan, wato shekara biyar baya, an sami ƙarancin masu nuna sha'awar karanta Hausa a matakin gaba da sakandare.

Har ila yau, wani babban ƙalubale da ya ke fuskantar harshen shi ne ƙarancin bincike da rubuce-rubuce a harshen. Kowane harshe da yake nema ya kai ga matsayin harshen hukuma, akwai bukatar ya zamanto an rubuce fannonin ilimi a cikinsa, wanda zai taimaka wajen koyar da fannonin ilimi a cikinsa. Abin nufi a nan shi ne, duk harshen da ba a zurfafa nazari a cikinsa da yawaita rubuce-rubuce na fagagen ilimi a cikinsa, zai yi wuya ya kai ga matakin harshen hukuma. Wannan ƙalubale ne da ya kamata masana da mahukunta da sauran al'umma su tashi tsaye domin ganin sun shawo kansa, tare da dawo da tsarin da ya dace da karantar da harshen a kowane mataki. Malamai su ƙirƙiro hanyoyin cusa sha'awar koyon

harshen ga ɗalibai. Mahukunta su bayar da dama ga nazarin harshen a kowane mataki ba tare da wani tarnaƙi ba. Gwamnati ta tallafa wa malamai da ƙarfafa masu gwiwa wajen koyarwa. Ƙungiyoyi da masu hannu da shuni su ɗauki nauyin bincike da fassara fagagen ilimi a harshen Hausa domin ciyar da ilimi da al'umma gaba, domin harshenmu shi ne abin alfaharinmu.

### 4.1.2 Kalubalen Kasar Hausa

Ƙasar Hausa a yau tana fuskantar babban ƙalubale na rashin kwanciyar hankali da rashin tsaro. Kowa ya san cewa noma shi ne ƙashin bayan tattalin arzikin ƙasar Hausa, amma a yau noma ya yi wuya saboda rashin tsaro. Haka kuma, kiwo da makiyaya ke yi yana taimaka wa ƙasar noma da samar da abinci. A yau, ta'addanci ya sa noma da kiwo suna nema su gagara a ƙasar Hausa. Daga cikin babban ƙalubalen da yake fuskantar ƙasar Hausa shi ne ruguza tsarin shugabanci da Bahaushe ya saba da shi wato tsarin mukuliya na sarakuna, da ɗaukaka tsarin shugabanci na dimakraɗiyya, wato shugabanci na gurguzu. Wannan tsari ya raunana ikon sarakuna tare da haifar da matsalolin rashin tsaro sakamakon kasa tantance tsarin shige-da-fice da yanayin zamantakewar al'umma. Malam Sa'adu Zungur yana cewa:

Ku fahimci shiri na Mulukiya,
Da yawan haɗarin Jumhuriya.
Sarki da gidajen shawara,
Da shari'a kun ji Mulukiya.
Mulki na wakilai gurguzu,
Babu sarki, babu sarauniya.
Sai 'yan sanda sai soja sai,
Oda ita ce Jumhuriya.
Fatarmu Arewa ta farga duk,
Don ta gane lamarin duniya.
(Sa'adu Zungur: Arewa Jumhuriya ko Mulukiya)

Wannan misali shi yake nuna halin da ƙasar Hausa ta shiga dangane da batun shugabanci. A yanzu an shiga yanayin da darajar sarakuna da ikonsu ya yi rauni, domin haka ba su da ikon zartarwa kamar yadda suke da shi a baya. Sakamakon haka, al'umma ta shiga yanayin ruɗani na shugabanci saboda tsarin da aka kawo ba ya biyan bukatar yanayin tsarin rayuwa na ƙasar Hausa.

### 4.1.3 Kalubalen Al'ummar Hausawa

Al'ummar Hausawa kamar sauran al'ummomi da suke bunƙasa a yau al'umma ce da take fuskantar gagarumin ƙalubale. Wannan ƙalubale kuwa ya bijiro ta fuskoki da dama kuma bisa dalilai da dama. Daga cikin ƙalubalen da ke damun wannan l'umma a yau shi ne taɓarɓarewar tarbiyya. Idan aka yi la'akari da yadda tarbiyya ta yi rauni, kyawawan ɗabi'u kamar gaskiya da kunya da kara da zumunci da kawaici duk sun yi ƙaranci a tsakanin al'ummar Hausawa a yau. A baya, waɗannan ɗabi'u sune suka yi fice a ƙasar Hausa, har ma aka shaida cewa Hausawa mutanen kirki ne, saboda riƙon da suka yi wa kyawawan ɗabi'u. (Kirk-Green, 1966).

A yau, samun waɗannan ɗabi'u a tsakanin al'umma ya yi ƙaranci. Munanan ɗabi'u irin su ha'inci da tumasanci da lalaci da ƙarya suna nema su maye gurbin kyawawan ɗabi'u, saboda masu aikata su suna nema su rinjayi masu aikata kyawawan ɗabi'u. Haka kuma, al'ummar tana fuskantar ƙalubalen shigowar baƙin al'adu sakamakon tasirin zamananci da wanzuwar shafukan sada

zumunta na zamani. Irin waɗannan baƙin al'adu sun yi tasiri a harkar zamantakewa na auratayya da maƙwabtaka da tattalin arziki da sana'o'i da sauransu. Al'ummar na neman guje wa waɗannan al'adu na asali, tare da maye gurbinsu da na baƙi kamar tsarin zamantakewar Turawa da sauransu. Kodayake masana da sarakuna da manya suna ta kira a kan kyautata al'adu da dawo wa tsarin zamantakewa da aka gada na kula da taimakon juna da sa ido a kan baƙin al'amurra domin magance rashin tsaro da shaye-shaye da sauran matsaloli da suka yi wa al'umma tarnaƙi. Malam Sa'adu Zungur dai yana cewa:

A Arewa zumunta ta mutu,
Sai nishaɗi sai sharholiya.
Sai alfahari da yawan ƙwafe,
Girman kai sai ƙwambon tsiya.
Camfe-camfe da tsibbace-tsibbace,
Maluman ƙarya 'yan duniya.
Cin amana kuma da yawan riya,
Ga hula mai annakiya.
Babu mai aiki bisa hankali,
Da basira don ya ga gaskiya.
Rantse-rantse da Allah yai yawa,
Ga ƙarya ga zambar tsiya.
(Sa'adu Zungur: Arewa Jumhuriya ko Mulukiya)

**5.1 Kammalawa**

Wannan muƙala ta yi waiwayen halin da Hausa ta samu kanta tun daga nasarori da matakin da ta kama, har zuwa ga matsaloli da ƙalubalen da suke fuskantarta. A ƙarshe, ana ganin cewa Hausa tana da kyakkyawar makoma da kuma ɗaukaka matuƙar al'ummarta suka tashi tsaye suka gyara matsalolinsu, suka dawo da martabar harshensu da kyawawan al'adunsu. Babu wata al'umma da za ta saki kyawawan ɗabi'u kuma ta yi nasara a rayuwa. Mafi yawan matsalolinmu suna nan danfara da riƙo da munanan ɗabi'u da al'ummar ta yi a yau. Akwai nauyi da ya rataya a yuwan kowane Bahaushe yaro da babba wanda ake bukatar ya sauke domin al'ummar ta ci gaba da amsa sunanta a doron ƙasa. Daga cikin wannan nauyi akwai amfani da harshen a kowane mataki, da nuna kishin harshen, da kiyaye kyawawan al'adu da al'ummar ta gada sa'annan zurfafa nazari da rubuce-rubuce a cikin wannan harshe domin koyar da fannonin ilimi a harshen.

**Manazarta**


Adamu, M. (1980). *The Hausa Factor in West African History*. Ahmadu Bello University Press in collaboration with Oxford University Press.

Adamu, M.T (1997), Asalin Hausawa da Harshensu. Kano: Ɗansarkin Kura Publishers Ltd

Abdulƙadir, Ɗ (1979), *Zaɓaɓɓun Waƙoƙin Da da na Yanzu*.Lagos: Thomas Nelson Ltd

Alhassan da Wasu. (1982), *Zaman Hausawa*. Zaria: Institute of Education.

Bakura, (2019) *Mulkin Mallakar Turawa a Ƙasar Hausa da Ginuwar Rubutaccen Labarin Hausa: Labarin Hausa a Rubuce*.Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Bugaje, H. M. (2014). "*Karin Magana Mahanga Tunani: Nazarin Lokaci a Hausa"*. Kundin Digiri na Uku, Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Bunza, A. M. (2006). *Gadon Feɗe Al'ada.* Tiwal Publishers.

Ibrahim, U. (2018). "Gudummawar baƙi 'yan kasuwa da fitattun sana'o'in Kanawa daga 1900–2015".Kundin Digiri na Uku: Zaria Jami'ar Ahmadu Bello.

Sani, A.-U., & Umar, M. M. (2018). Global growing impact of Hausa and the need for its documentation. Contemporary Journal of Language and Literature, 1(1), 16–34. http://sgpicanada.com/index.php/CJLL/issue/download/1/Abu-Ubaida%20Sani%20and%20Muhammad%20Mustapha%20Umar

Sani, A-U., Buba, U. & Mohammad, I. (2019). Wanda ya tuna bara...: Biɗa da tanadi a tsakanin Hausawa matasa a yau. Global Academic Journal of Humanities and Social Sciences, 1(2), 44-50. www.doi.org/10.36348/gajhss.2019.v01i02.001.

Tahir, R. M. (2024). Tsaro da sarauta a Bahaushiyar Al'ada. Muƙalar da aka Gabatar a Taron Makon Hausa, Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello

Vycichl, W (1934), Hausa and Egyptian. (Translated by Paul F. 2002),

Yahaya, I. Y. (1988). *Hausa a rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa.* Zaria: Kamfanin Gaskiya.